# Littafi mai Tsarki na yara

## Ke gabatar da

# Bai-bai Firauna



**Wanda ya Rubuta: Edward Hughes**

**Mai Zane: Janie Forest**
**Alastair Paterson**

**Mai niyyan daukan nauyi: Lyn Doerksen**

**Fassarawa: Bible Society Nigeria**

**Wanda ya Wallafa: Bible for Children**
**www.M1914.org**

**©2024 Bible for Children, Inc.**
**Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan**
**har ba zaku sayar da shi.**



**Firauna ya yi fushi! Allah ya umarce shi ta wurin Musa domin ya bar bayin nan Isra’ilawa su bar Masar. Ya ki. “Ku sa suyi aiki cikin tsanani,” Firauna ya umarce masu lura da bayin. Yanzu abubuwa sun kara tsanani wa Isra’ilawa.**

**“Ku tattara karanku da kanku.  Ba za mu ba ku su kuma ba.  Amma za ku buga bulok daidai yawan da kun saba bugawa.”  Wadannan ne sabobin umarnan Firauna.**



**Masu lura da bayin sun bulalle wadansu bayin saboda ba su tattara kara na gini da bulok ba.**





Mutanen suka sa wa Musa da Haruna laifi saboda damuwoyinsu. Musa ya nemi wuri ya yi addu'a. "Ya UBANGIJI," ya yi kuka, "Ba ka kubutar da mutanenka ba ko kadan."

"Ni ne UBANGIJI, kuma zan fitar da ku," Allah ya amsa.

**Sa’an nan Allah ya sake aikan Musa da Haruna zuwa wurin Firauna. Sa’ad da babba mai mulki ya tambayi ‘yan hidimar Allah alama daga wurin Allah,**

**sai sandan Haruna ya canja zuwa wani maciji mai walkiya.**





**"Ku kira mini masu duba na," Firauna ya yi ihu. Sa'ad da suka jefar da sandunansu, kowane sanda ya zama maciji shi ma. Amma sandan Haruna ya hadiye sauran. Duk da haka, Firauna ya ki ya bar mutanen su tafi.**

**Washegari, Musa da Haruna suka sadu da Firaunaa a bakin kogi.  Sa’ad da Haruna ya mika sandansa, Allah ya canja ruwan zuwa jini.  Kifaye suka mutu.  Mutane ba su iya shan ruwan kuma ba.**



**Amma Firauna ya taurara zuciyarsa. Bai yarda ya bar Isra’ilawa sun bar kasar Masar ba.**





**Kuma, Musa ya sake fada wa Firauna ya bar mutanen Allah su tafi. Firauna ya ki kuma. Allah ya sake aika wa da wani annoba. Ko’ina a Masar ya cika da kwadi. Kowane gida, kowane daki, har ma wuraren dafa abinci, ko’ina kwadi!**



**“Ka yi mini addu’a, domin Allah ya cire kwadin,” Firauna ya roka. “Zan bar mutanenka su tafi.” Amma, bayan da kwadin suka tafi, Firauna ya canja ra’ayinsa. Ya ki ya bar bayin su sami ‘yancinsu.**

**Allah ya sake aika wa da kananan kwari masu cizo da yawa. Kowane mutum da dabba jikinsu yana kaikaiyi daga cizonsu, amma duk da haka Firauna ya ki ya yi biyayya ga Allah.**





Biye da shi sai Allah ya aiko da kuda, a kungiyoyinsu. Allah ya aika cututtuka suka kashe dabbobin Masarawa. Allah ya aika da kuraje masu zafi. Mutane suka sha azaba sosai. Duk da haka Firauna ya ki ya yi biyayya ga Allah.





Bayan annoban mikoki, Allah ya aika da rundunar fari. Sai farin suka cinye kowane iri amfanin gona na kasar.



**Sai Allah ya aika da duhu gaba ki daya na kwana uku.  Amma duk da haka Firauna mai taurin kai ba zai ‘yantar da Isra’ilawa ba.**

**“Zan aiko da annoba guda daya kuma,” Allah ya ja musu kunne. “Da tsakar dare, duk dan fari mutu da dabba zai mutu.” Allah ya gaya wa Isra’ilawa ‘ya’yan farin su zasu tsira idan sun saka jinin rago a kofan saman kofansu.**





Da tsakar dare, kuka mai karfi ya barke a cikin Masar. Mutuwa ta kai hari. A Kalla, mutum daya ya mutu a kowane gida.





**“Ku fita,” Firauna ya roki Musa.  “Tafi, yi wa UBANGIJI hidima.” Nan da nan mutanen Allah suka bar iyakar kasar Masar.**



**Allah ya gaya wa Musa ya tuna da Daren Faska saboda Mala'ikan Allah ya wuce a bisan gidajen Isra'ilawa ya kuma kai wa Firauna hari da shi da mutanensa.**



Bayan shekaru 430 a Masar,
mutanen Allah yanzu suna
da ‘yanci.  Allah ya bi da su
da tulin hadari da rana,
da tulin wuta da dare.



**Amma Firauna bai gama da Isra’ilawa ba. Ya sake mantawa da Allah. Kuma, ya canja ra’ayinsa. Sai ya tattara sojojinsa, ya bi bayan bayin. Ba a dadde ba, sai ya sa aka kewaye su tsakanin gangara da teku.**



**“UBANGIJI zai yi fada a madadinku.” Musa ya ce. Musa ya ci gaba da tafiya har bakin ruwa, sai ya mika hannunsa.**



**Babban al’ajibi ya faru. Allah ya bude hanya a tsakiyar ruwan. Mutanen suka ketare lafiya lau.**

Sa’an nan sojojin Firauna suna ta kai da kawowa a cikin Kogin Ciyawar Iwa. “Yanzu za mu kama su,” sojojin suna tunani. Amma Allah ya rufe ruwayen. Haka aka hadiye wannan sojojin Masar masu iko. Yanzu Firauna ya sani cewa Allahn Isra’ila shi UBANGIJI ne a kan kome.



# Bai-bai Firauna

## Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

## a na samu a

## Fitowa 4-15

**"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130**

# KARSHE

11

60

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**